## Addu’a da Furuci game Rudi

*Uba, ina yi maka godiya domin kai Allah ne na gaskiya, kana haskaka hasken ka a cikin duhu mafi baki. Yau na zabi in fita daga cikin duhu, in kuma zauna a cikin haskenka.*

*Idan ka yarda ka gafarta mani karairakin da na yi. Sau da yawa na zabi hanyar jin dadi wadda take mai sauki a maimakon wadda take daidai. Ina rokonka ya Ubangiji ka wanke lebunan baki na daga kowace rashin gaskiya. Ka bani zuciya wadda take farin ciki da gaskiya, da kuma baki wanda yake a shirye domin ya sanas da gaskiya ga wadansu.*

*Ka bani karfin halin jin dadin gaskiya da kuma kin karya.*

*A yau ina kin karya, ina zubas da dukan karya daga cikin rayuwa ta.*

*Ina yin watsi da dukan koyaswar Musulunci wadda ake amfani da it domin a baratas da karya, wannan kuwa ya hada har da* taqiyya. *Na zabi in juya wa karya da rudi baya. Na zabi in yi rayuwa a cikin gaskiya.*

*Ina furta cewa Yesu Kristi shine Hanya, shine Gaskiya, shine kuma Rai.*

*Na zabi in yi rayuwa a karkashin kariyar gaskiyarsa*

*Ina furta cewa kariyata a cikinka take, kuma gaskiya zata yantas da ni*

*Ya Uba na sama, ka nuna mani yadda zan iyi tafiya a cikin hasken gaskiyarka. Ka bani kalmomin da zan ambata da kuma hanyar da zan yi tafiya a ciki, wadda take kafe a cikin gaskiyarka.*